# KISSAR FARKARWA

Dubi Cikin
Rayuwar Ilmi da Siyasa Ta Imam Khumaini (R.A)

(Daga Haihuwa Zuwa Rasuwa)

HAMID ANSARI

Cibiyar Bincike da Wallafa Ayyukan
Imam Khumaini (r.a)
(Sashin Harkokin Kasashen Waje)

www.ketab.ir

انصاری، حمید، ۱۳۳۵ ـ
حدیث بیداری: نگاهی به زندگینامه آرمانی، علمی و سیاسی امام خمینی (از تولد تا رحلت). هوسایی (کیسار فارکاروا: ...)/ نویسنده حمید انصاری، ترجمه محمداول برچی. ـــ تهران: مؤسسه تنظیم و نشر آثار امام خمینی(س)، ۱۳۸۶. ۲۰۲ ص. : مصور(بخشی رنگی).

ISBN: 964 - 335 - 794 - 5

فهرستنویسی براساس اطلاعات فیپا.
هوسایی. کتابنامه: ص۲۸۱ ـ ۲۰۲.
۱. خمینی، روح‌الله، رهبر انقلاب و بنیانگذار جمهوری اسلامی ایران، ۱۲۷۹ـ ۱۳۶۸. ـــ ـ سرگذشتنامه وکتابشناسی. الف. مؤسسه تنظیم و نشر آثار امام خمینی دفتر معاونت امور بین‌الملل . ب. اول برچی، محمد، مترجم. ج. عنوان.

۲۰۲۹۹ ح ۸ الف/ DSR ۱۵۷۶ ۹۵۵ / ۰۸۴۲۰۹۲
کتابخانه ملی ایران ۸۴ ـ ۴۱۶۷۰ م

کد / م ۲۰۰۵

Kissar Farkarwa
Dubi Cikin Rayuwar Ilmi da Siyasa Ta Imam Khumaini (R.A)
**Wacce Ta Buga**: Cibiyar Bincike da Wallafa Ayyukan Imam Khumaini (r) Sashin Harkokin Kasashen Waje
**Mawallafi**: Hamid Ansari
Mai Fassara: Muhammad Awwal Bauchi
**Shekarar Da Aka** Buga: 2007
**Adadi**: 1500
**Farashi**: 58000 Rl.
**Adireshi**: No. 5, Sudeh Alley, Yaser St., Shahid Bahonar Avenue, P.O. Box 19575-614 Tehran-19776, Iran.
Tarho: (+9821) 2229 0191, 2228 3138
**Fax**: (+9821) 22874072, 2229 0478
Email: pub@imam-khomeini.ir
Shafin Internet: www.imam-khomeini.org

(حدیث بیداری به زبان هوسائی )

# ABUBUWAN DA KE CIKI

Gabatarwa ....................................................................9
Shimfidar Tarihi:..............................................................12
Imam Khumaini: Daga Haihuwa Har Hijira Kum: ........15
Hijira Zuwa Kum Don Karatu da Karantarwa: .............18
Imam Khumaini a Fagen Gwagwarmaya:.......................22
Yunkurin 15 ga Khordad (5 ga Yuni): ..........................59
Adawar Imam Ga Dokar Kare Amurkawa da Korarsa Turkiyya:.........................................................................71
Hijira Daga Turkiyya Zuwa Iraki: ................................79
Kungiyoyi da Jam'iyyun Siyasa ....................................95
Imam Da Ci Gaban Gwagwarmayar (1971-1977) .......105
Kololuwar Juyin Musulunci da Yunkurin Al'umma: ...112
Hijirar Imam Daga Iraki Zuwa Paris...........................117
Dawowar Imam Khumaini Gida: .................................122
Faduwar Hukumar Shah da Nasarar Juyin Islama .......129
Kafa Hukumar Musulunci:...........................................132
Juyi Na biyu; Kame Ofishin Leken Asirin Amurka A Tehran: .........................................................................141
Kallafaffen Yaki: Shekaru Takwas na Kariyan Kai:....160
Me Ya Sa Yakin Ya Ci Gaba: ......................................167
Albishirin Faduwar Cibiyar Markisanci Ta Duniya Cikin Sakon Imam Ga Gorbachev: ........................................185
Kariya Ga Manzo Da Kuma Akidun Addini: Karshen Kace-Nacen Imam Da Kasashe Yammaci: ..................187
Shekarun Karshe Na Rayuwar Imam da Ababen Bakanta Rai Da Suka Faru: ......................................................189
Dubi Cikin Akidu Da Manufofin Imam:......................207
Wafatin Imam: Rabuwa da Masoya Da Haduwa Da Abin Kauna: .........................................................................236
Rubuce-Rubucen Imam Khumaini:..............................252
Karin Bayani: ..............................................................281

www.ketab.ir

## GABATARWA

A cikin wannan aiki (rubutu) dai, an yi ƙoƙarin yin kammalallen bayani duk da cewa a taƙaice ne kan rayuwar (marigayi) Imam Khumaini (r.a) tun daga haihuwa har zuwa rasuwa. Bayani kan rayuwar Imam Khumaini da irin abubuwan da ta ƙunsa na falala da ɗaukaka cikin wata 'yar maƙala ko kuma ƙaramin littafi (kamar wannan) tamkar zuba ruwan kogi ne cikin wata 'yar kwalba, to amma duk da haka za mu yi iyakacin ƙoƙarinmu wajen gabatar da wani abu musamman ma saboda buƙatar da masoya Imam a sauran ƙasashen duniya suka nuna na a gabatar musu da wani abu kan rayuwarsa. To sai dai duk da haka mun yi ƙoƙarin taƙaita bayani kan abubuwan da muka yi magana a kansu face a guraren da buƙatan hakan ta zamanto tilas; duk da cewa mun yi iyakacin iyawanmu, ko da kuwa a taƙaice ne, wajen taɓo duk wani abin da ya shafi Imam Khumaini ko kuma wani abin da ya share fage wajen wannan yunƙuri nasa.

A daidai lokacin da muke ƙoƙarin bayani kan abubuwan da suka faru a rayuwar Imam Khumaini, mun yi ƙoƙarin ba da muhimmanci kan irin ingancin aƙida, ikhlasi da ƙarfin ilmi da kuma tasirin da ilmi da tsoron Allah suka yi cikin rayuwarsa da kuma tafarkin da ya ɗauka.

Kamala da cikar da shaksiyyar Imam Khumaini da aƙidarsa suke da shi, su suka sanya yunƙuri da juyin juya halinsa suka kasance sama da wani canji na wata

al'umma ko ƙasa guda, su suka sa ake buƙatuwa da nazari cikin dukkan ɓangarori na rayuwarsa ba wai kawai wani sashi na rayuwar ba. Don haka wannan aiki wani ƙoƙari ne a wannan ɓangare.

Daga ƙarshe mun yi ƙoƙari wajen ganin duk wata natijar da za mu fitar daga ƙarshe ta yi daidai da haƙiƙanin abubuwan da suka faru da kuma irin tunani da koyarwa ta mai girma Imam Khumaini. To sai dai duk da haka babu yadda za a iya cewa babu 'yan kura-kurai cikin wannan aiki. Don haka muke buƙatan masu karatu da sauran masana tarihi da su jawo hankulanmu zuwa ga gazawa da kura-kuran da za su iya gani.

*Hamid Ansari*
*Azar 1373*

www.ketab.ir